BU African Studies Center LANGUAGE PROGRAM, 232 BAY STATE ROAD, BOSTON, MA 02215 africa@bu.edu
www.bu.edu/Africa/alp 617.353.3673

## *Skit 3: Saki jikinka ɓarawo a hannun mata.*

| | |
|---|---|
| Yazi Dogo: | **Lalle! Ma'anar wannan karin magana shi ne girma ya hwaɗi.** |
| A1: | ***Ku bari dai mai saukita inda kun bi ni da mun samani.*** Yahaya na ni ce maka, Yaji ya yi barka, ya yi sa'a wallahi. Ka duba jiya abun da an kai. Kai ɗan karen gudu da a gareshi wannan abu kai … Mu da kyat munk… Kai bai cimmuwa. |
| A2: | A, ba ya cimmuwa! Ina! Ai ba …. |
| A3: | To ni ka san yadda su kai min? |
| A2: | E! |
| A3: | Da ni zo daga gari, sai ni yi yal miyan nan tawa, da ɗan buruna, na sha, sai na shiga ɗaki, kawai sai na ɗan kara ƙyaure irin wannan. |
| A2: | Mmm. |
| A4: | Ka ga … |
| A3: | Kawai na gaya ma sai suka zo suka janye mini **parparo**. Yanzu ma a ƙahwa ni ke. |
| A4: | A, a, abun da ban so ba, **hwada**r nan kullum in muka zamna, maimakon ku rika zancen harakal kuɗi, kuɗi wanga **harakokin kasuwanci** … |
| A2: | To an ɗauke mishi moto ba kuɗi zai sayi moton ba? |
| A3: | An ɗauke min moto ko …. kyauta aka ban moton? |
| A4: | To kullum zance guda, zancen ɓarawo dai … |
| A2: | To. Yau! Shi ya mumu ciwo manan! |
| A3: | Lokacinshi ne ya zo! |

© Boston University

A4: Mai ƙarhi yake yin sata! Da zuciya!

A2: Ee. To mun ji mai ƙarhi yake yin sata. Amma ...

A1: Ba shi ba ne!

A4: In ka rasa aikin da zaka yi ba sai sata ba?

A1: A'a. Ba shi ba ne!

A2: To amma dai in an yi ma mutum zai ji zahi ko?

A3: Sai a sace min moto, ba na yi magana ba?

A2: To, to, ka ji ko? Ka ji wata magana ta banza da wohi?

A4: To ku yi ta hirar ku mu yanzu...

A3: Kai amma dai **waɗanga** mutane ba **mutanen arziki** kuke ba!

A4: Mu zancen kasuwanci muke so.

A2: To ku tahi ku yi ta kasuwancin! Ku tahi ku yi ta kasuwanci!

A1: Kai ko ana zance, mutane suna da matsala.

A3: A yi muna sata ka ce ba ma yi magana ba?

A2: A, ai ba ka gane ba. Ɓarawon nan na Yaji da muka kora jiya,

A3: Mmm.

A2: Ni dai in ba dan tsoron Allah ba da harakar **duhu**, ni...kai ni da na ce shi ne.

A3: Ee.

A5: Kai, wane ne? Wane ne nan?

A1: Wanga?

A2: I. Dan dai harakar duhu ce **mutum ba ya da tabbat**. Amma ni dai kai dai, to ...

A3: To ni in ba haka nan ma, mi ya sa Kalla da ka yi zance, zai kwaɓe ka ya ce don mi kake zancen ɓarawo?

A1: Kai tsaya! Tsaya! Kai! Kai! Ba **ihu** kuke ji ba? Ba ku jin ihu can?

A2: Kai ko "accident" ne?

- Kai ɓarawo, Allah ya kama ka!

A1: Ɓarawo aka cewa. Kai ku tashi mu tahi zancen ɓarawo na! Ku tashi mu tahi, zancen ɓarawo na a kai.

- Ɓarawo ne nan!

- Yau mun kama ɓarawo! Allah ya kama ka!

Ɓarawo (Ɓ): Ke tsaya!

- A tsaya wa? Uban wa?

Ɓ: Tumkiyata! Tumkiyata!

- Tumkiyar wa?

Ɓ: Ta yi kama da tawo!

A6: Kai! Ke! Ke, ke, ke! Ke tsaya ke! Kai! Bari, bari! Ku bari!

- Haba tsoho? Ɓarawo na!

- **Munahuki**n Allah!

A6: Yanzu kai ne nan wurin? Tsaya kai! Ku dakata dan Allah na ce muku! Mi ya kawo ka nan kai?

| | |
|---|---|
| | - Ɓarawo na! Ɓarawo. |
| Ɓ: | Allah dai in ya kawo abu. Tumkiyata ce ta ɓace. Sai |
| | - I. |
| Ɓ: | Sai na biyo sai na ga irinta. |
| | - Ko kwanakin can kai uku ya tare, kuma yanzu ya komo ya tare wasu. |
| | - **Karya** yake ɓarawo na. Ya daɗe ya na yi |
| A6: | Don Allah ku yi mishi a hankali! |
| Ɓ: | Ba ka gani mata ne. Mata ne. |
| A6: | Na sani. Ku bari dan Allah! Kai, kai! |
| A3, A1: | Kai lahiya? |
| Ɓ: | **Tsotsai**! |
| | - Tsotsayin Ubanwa? Karya! |
| Ɓ: | **Tumkiya**ta ta ɓace aka ce ta shigo nan. |
| | - Karya! Tumkiya uku ta ɓace muna. |
| | - Karya yake! |
| | - Tumkiya uku ta ɓace, ashe shi na! |
| | - Yau dai Allah ya kama |
| A2: | Kai, kai, ba kun ga zancena ba? |
| A3, A1: | Zancenka ke nan. |
| A2: | Ba kun ga zancena ba? |
| A1, A3: | Zancenka ke nan! Ɓarawo ga hannun mata. Ku bari, ku bari! Ya isa! Muna tahiya da shi. |

| | |
|---|---|
| | - A bari |
| | - Dan Allah ku tuɓe muna shi. |
| A1, A2, A3: | A’a. Ku yi haƙuri! Dakata! |
| | - Ɓarawo! |
| A6: | Ku **tuhwa mishi asiri**! |
| A1, A3: | Ku bari, ku yi haƙuri! |
| A6: | Ku tuhwa mishi asiri! |
| | - Na kiya! |
| All men: | Ku yi haƙuri! |
| | - Munahukin Allah! Ɓarawon banza. |
| | - Yau Allah ya kama ka. Asirinka ya |
| | - Ashe, kai ɓarawo ke nan mai kama tumakin mutane. |
| | Allah ya toni asirinka. |
| All men: | Ku yi haƙuri! |
| | - Ɓarawo, ɓarawo! |
| | - Ka **ba maza kumya** na **rance da Allah** yau! |
| | - Ka tai ka biɗi abin da ka ci da mutane. |
| | - Munahukin Allah! |
| | - Asi |